# Fiqihun ibada a cikin hotuna

## Karantar da hukunce-hukuncen musulunci a sauqaqe

Tsarki | Sallah | Azumi | Zakkah | Hajji



د. عبدالله بن سالم باهمام

tarjama

Muhammad Rabi'u Umar Musa R/lemo

bita

Dr. Muhammad Sani Umar Musa
Shaikh Nura Sani Muhammad

## Lailatul Qadari

Abubuwan Da Ke ciki

Me Ya Sa Aka kira shi da lailatul Kadari
Falalar Daren Lailatul Kadari Da Matsayinsa
Wane Dare ne Daren Lailatul Kadari?
Ayyukan Da Ake Son Yi A Daren Lailtul Kadri
Alamomin Daren Lailatul Kadri

## Me Ya Sa Aka Kira Shi Da Lailatul Kadri

1 – An ce, saboda girmamawa (saboda kalmar Kadru a larabci tana nifin girma) kamar faɗin Allah Maɗaukakin Sarki "Ba su girmama Allah iyakar girmamawa ba". (Al-An'am : 91) Abin da ake nufi, wannan dare ne mai girma, saboda Alƙura'ni ya sauka a cikinsa, da kuma abin da yake faruwa na saukar Mala'iku da Albarka da Rahama da gafara a cikinsa".

2 – Wasu kuma suka ce, Alƙadru, yana nufin ƙuntatawa, kamar yadda Allah ya yi amfani da wannan kalmar da wannan ma'ana inda yake cewa "Wanda aka ƙuntatawa arzikinsa ya ciyar daga abin da Allah ya ba shi". (Aɗɗalaƙ : 7) Abin da ake nufi da ƙuntatawa a cikin wannan dare, shi ne ɓoye daren da aka yi, ba a bayyana shi ba.

3 – Wasu suka ce, "Alƙadru a nan, yana da ma'anar "Alƙadaru" wato ƙaddara, saboda abin da ake ƙaddara wa na shekara cikin wannan dare, don Allah Maɗaukakin Sarki ya ce, ""A cikin wannan dare ne ake rarrabe dukkan wani lamari hukuntacce. (Addukhan : 4).[1]

(1) **Fathul- Bari (4/255).**



https://www.al-feqh.com/ha/category/azumi

https://www.al-feqh.com/ha/category/azumi

## Falalar Daren Lailatul Kadari Da Matsayinsa

### 1 – A Cikinsa Ne Aka Saukar Da Alƙur'ani

Allah ya ce, "Haƙiƙa Mun saukar da shi a cikin daren Lailatul Kadri" (Alƙadri : 1).

### 2 – Ya Fi Wata Dubu

Allah ya ce, "Daren Lailatul Kadari ya fi wata dubu alheri" (Alƙadri : 3). Ma'ana aiki a cikin wannan dare ya fi aikin wata dubu ba a daren Lailatul Kadari ba.

### 3 – Mala'ika Jibril Da Sauran Mala'iku Suna Sauka A Cikinsa

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce, "Mala'iku da Mala'ika Jibrilu suna sauka a cikinsa da izinin Ubangijinsu daga kowane lamari" (Alƙadri : 4).

An kaɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, "Daren Lailatul Kadari shi ne daren ashirin da bakwai ko ishirin da tara. Mala'iku a wannan daren sun fi yawan tsakuwa a bayan ƙasa"[1].

### 4 – Dare Mai Aminci A Cikinsa

Allah Mai Girma Da Buwaya ya ce, "Aminci ne a cikinta har zuwa ɓullowar alfijir". (Alƙadri : 5) Ma'ana dukkan wannan dare alheri ne, babu wani sharri a cikinsa tun daga farkonsa har zuwa ɓullowar alfijir.

### 5 – Dare Ne Mai Albarka

Allah ya ce, "Haƙiƙa mun saukar da shi a cikin dare mai albarka. Haƙiƙa mu masu gargaɗi ne". (Addukhan : 3). Abdullahi ɗan Abbas ya ce, "Yana nufin daren lailatul Kadri".



(1) **Ibn Khuzaima ne ya rawaito shi**

## 6 – A Cikinsa Ake Kaddara Dukkan Abubuwan Shekara

Allah ya ce, "A cikinsa ake rarrabe kowanne lamari abin hukuntawa" (Addukhan : 4).

## 7 – Wanda Ya Yi Kiyamullaili Yana Mai Imani Da Neman Lada To Za A Gafarta Masa Abin Da Ya Gabata Na Zunubinsa

Manzon Allah ﷺ ya ce, "Wanda duk ya yi tsayuwar daren Lailatul Kadri yana mai imani da neman lada, an gafarta masa abin da ya gabata na zunubansa"[1].

## Wane Dare Ne Lailatul Kadri

Allah ya ɓoye wannan dare don musulmi ya yi ƙoƙari da himma a goman ƙarshe ta Ramadan, musamman ma a dararen da suke mara, waɗanda su ne daren 21, 23, 25, 27, 29, saboda faɗin Manzon Allah ﷺ "Ku kintaci daren Lailatul Kadri a cikin marar goman ƙarshe ta Ramadan"[2].

Wasu malamai sun yi bayanin cewa daren Lailatul Kadri yana yawo a tsakanin waɗannan darare (Wata shekarar wannan, wata shekarar wancan) saboda a yi aiki da dalilan da suka zo a kan haka baki ɗaya.

## Ayyukan Da Ake Son Yi A Daren Lailtul Kadri

1 – I'itikafi : Ana yinsa ne a goman ƙarshe a Ramadan, ba sai a daren Lailatul Kadri kaɗai ba. An karɓo daga Aisha – Allah ya yarda da ita – ta ce, "Manzon Allah ﷺ ya kasance yana yin I'itikafin kwanaki goma na ƙarshe a Ramadan"[3].



(1) Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi
(2) Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi
(3) Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi

2 – Tsayuwa a wannan dare don imani da neman lada : Manzon Allah ﷺ ya ce, “Wanda ya yi tsayuwa daren Lailatul Kadri yana mai imani da neman lada, an gafarta masa abin da ya gabata na zunubansa”[1].

3 – Addu’a : An karɓo daga Aisha – Allah ya yarda da ita – ta ce, na ce, ya Rasulallahi, idan na dace da daren Lailatul Kadri, me zan yi addu’a da shi? Sai ya ce, ki ce, “Allahumma Innaka Afuwwun Karimun Tuhibbul Afwa Fa’afu Anni” Ma’ana “Ya Allah kai mai afuwa ne mai karamci, kana son afuwa, ka yi min afuwa”[2].

## Alamomin Daren Lailatul Kadri

### 1 – Dare Ne Mai Haske, Babu Zafi Ko Sanyi A Cikinsa

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi – Allah ya yarda da shi – ya ce, “Haƙiƙa ni an nuna min daren Lailatul Kadri, sannan an mantar da ni shi, yana goman ƙarshe na Ramadan, dare ne babu sanyi ko zafi a cikinsa, kuma mai haske ne, ba zafi ba sanyi (mai cutarwa a cikinsa)[3].

### 2 – Rana Tana Fitowa Da Safiyar Daren Fara Tas Ba Haske Tare Da Ita.

Yayin da aka tambayi Ubayyu ɗan Ka’abu – Allah ya yarda da shi – a kan alamomin daren Lailatul Kadri, sai ya ce, “Alamar da Manzon Allah ﷺ ya ba mu labari ita ce, rana tana ɓullowa a wannan rana babu haske tare da ita”[4].



(1) Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi
(2) Tirmizi ne ya rawaito shi.
(3) Ibn Khuzaima ne ya rawaito shi
(4) Tirmizi ne ya rawaito shi